**Ma' aikatar Ministan Guidan Gona**

**PROJEN VRACS**



**L I T T A H E N  B A D A  H O R O  B I S A  T A T T A L I N  D A M**

**2015**

LITTAHEN BADA HORO BISA TATTALIN DAM


I. **Gabatarwa** 3

II. **Gurin horo** 3

III. **IIISakamako da ake jira** 3

IV. **Masaloli da dam ke fuskanta**

## I. Gabatarwa

A cikin tsarin ayukanshi, Puroje mai kula da bincike - bincike don bunkasa ayukan noma a cinkin fadamu na cikin yankin Sahel (EDOS) yayi niyar taimakama mazamna karkara ta hanyar daman kula dadam a cikin garuruwan: Burdi (Illela), Eduk (Cintabaraden), Gidan bado (Buza) da Jaja(Tawa).

## II. Gurin horo

Gurin da ake nema a cimma ta hanyar horo shine bada dama ga masu ma akaitan dam domin su samu masaniya ayukansu na gyara da kula dam yaw da kullum misali :

- Kishin gyabbu
- Kula da hitar duwatsu da ga dam
- Sassaben kananan itace
- gyaran wuri ginnanne
- gyaran wayoyinda da su ka katse na dam dasaouransu
- etc.

## III. Sakamako da ake jira

- Muatane su gane da anfani kula da dam
- Mazamnan horo su gane huso o in kare dam
- Mazamnan horo su bada fasalin bisa ayyukar kare dam.

## IV. WASU BAYANAY SAMAN DAM

### 1. Kwatamci

- **Karamin dam**

Karamin dam wani guini da aka guina tsakan hanyar ruwa domin taré gudanar ruwan masu fotowa daga tudu domin tariyar su a dindindin ko tsawon wani lokaci domin ayuka masu dama ko na masaman.

- **Madatsar ruwa**

Shi ma wani guini né da aka guina tsakar hanyar ruwa domin tsaida gudanar ruwa daga tudu aman bambanci shi da karamin dam, yana baza ruwan né domin karin ruwa a karkashin kasa.

### 2. Fasalin karamin dam da madatsar ruwa

Iraran dam da madatsar ruwan da aka saba yi a jahar su né :

- Guini marufar dam;
- Gabobin guefe (mafitar ruwa da wani lokacin, makolhar ruwa da matarar ruwa).

#### 2.1. Guini marufar dam

Wani babban guini né da ruwa basu ratsawa da aka yi da kasa daddalalla mai fadi daga kasa da fadin saman da batakai ta asa ba, fadin saman yana mita 3,5 da gangara zoua daga saman chi. Guinin dam in yana da makoncin mai gudanar da ruwa zuwa kasa a wuraran da tsayin ruwan yafi mita uku (3). An tanadar da makarar jikin dam in da saman chi domin karé chi daga batchéwar shi ire ire.

#### 2.2. Gabobin guefe

Sassan guefe wasu gabba ne da aka yin domin tchika wasu ayuka na massaman masu nassaba da unfani da ruwan da aka tara, ko masu nasaba da kiyaye war madatsar.

⇒ Mafitar ruwa : wasu gabba ne na tsaro da aka yi saman madasun ruwan da uma saman kan'kanan dam domin su tabatar da fitar ruwan da suka yi yawa yanda ya dace da kuma tara su a kasan dam in. Akoye mafitar ruwa iri iri, wanda aka hi gani saman kankanan dam da madatsar ruwan su ne wa inda ke da abubuwan da ke tafe (dam da aka yi da dutsi) :

- baki ;
- bancin cika ;
- Hilin yada ruwa a kassan bancin cikan ;
- karamin  Banci;
- Tarin duwa tsu da
- Bangwayan guefe.

Dangane da kayan guini, akoye mafitar ruwan da aka yi da karfafan kankare, da duwatsuna, da guinin dutsi, da dutsina a cikin waya da mai gamin irare dayawa.

⇒ Madatsun fitar da ruwa : An yi su né domi fitar da ruwa, kadan ko dukan su a lokacin da madatsar ke fuskantar barazanar lalacéwa kokuma wani halin dake iya tchutar da dam in ko wani guefan sa. Ana iya anfani da shi domin rague ruwa kokuma dukan su dan shirya gonnakin noman rani.

⇒ Ma jayar ruwa : su na koumche ne da tiyouyoukan jan ruwa, ko wa insu na'urey na kurya masu gabban shirya aiki (na'urar jan ruwa, mafitar ruwa, marifa, makoncin ruwa,

da hanya…)

## V. SAKA IDO AKAN KANANAN DAM DA MADATSUN RUWA

### 1. JEWAYA TA YAW DA KULLUM

Manufar ta shi ne lura, a gaggauce, da duk wani sabon abunda kan iya hadassar da matsala akan dam in da kuma cigaban shi. Abubuwan dubawa :

- Bayyana ko yaduwar wurare masu dan dangni saman guini ko a kasan dam ;
- Bayyana ko yaduwar hudodi guraran gangarar dam ;
- Toushewar tiyouyouka ;
- Houdodin wuri wuri, wa'inda suka bayana a gangarar da aka daddale, da suke tafiya da kasa ;
- **Houdodin boude ko na rufe masu fitar da ruwa ko wa'inda basu fitar da ruwa;**
- **Tushewar mafitar ruwa da wa'insu aboubuwa saman ruwa.**
- **Zaizayewar guini na sam ko na kasan dam ;**
- **Korri a saman da aka daddale ;**
- **Fitowar itatuwa a saman dam ko kasan shi ;**
- **Yaduwar itatua a saman duwatsu na tcikin wayoyin.**
- **Gurbacewa ginin dutsin sama (fitar duwatsu, zaiayewar su …) ;**
- **Tsatsa ko tcirewar wayoyin kegi ;**
- **Tashi ko tsagewar shafe.**

### 2. Abubuwa lura a sakamakon yawan ruwa

Lokatcin karuwan ruwa ne dam suke fuskantar matsin lamba mai dama : hayewar ruwa, yawan ruwan daké gangarowa saman mafitar ruwan, gudanar ruwa akan shafe…

#### 2.1. Abubuwan lura loacin yawan ruwa

- Yawan ruwa matsakaici ;
- Jimawar yawan ruwa ;
- Aikin magudanan ruwan, yanayin ruwan, gunar ruwa saman magudar ko saman duwatsu ;
- **Yuwuwar Kewayewar bangwayen gefe ;**
- **Gudanar ruwa saman dam.**

#### 2.2. Abubuan lura bayan yawan ruwa

- Tsayin yawan ruwa saman magudanar ruwa dalillin wasu ma'aunai kamal shedan wutcewar ruwa, ajiar reshinshikan itace ...
- **Halin magudanar ruwa da mayadar ruwan ;**
- **Aiayewar kasa ;**
- **Hadewar dam da ginin sabilin ruwa ;**
- **Zaizayewar saman dutsi da kasan dam ;**
- **Zaiayewar gindin dam ko na guinin bango ;**
- Bayanar sabi houdodin fitar ruwa ko karin girman tsohin houdodin fitar ruwa.
- **Kewayewar bangwaye dam ;**
- **Zaizayewar kasa guindin dam ;**


- **Fitar duwatsuna ;**
- **Zamnewar duwatsuna ;**
- **Tcirewar wayoyi ;**
- **Fitar kayan tsakanin kasa da duwatsunan tcikin keji...**

## VI. DALILLAN LALACEWAR DAM

1. Gunarar ruwa ;
2. Rashin tsarin duwatsuna ;
3. Fitowar itace saman shi ;
4. Lalacewar ginin ;
5. Lalacewar duwatsunan cikin keji ;


Taruwar kasa da cikewar wuri.

a. Masaloli da dam ke fuskanta




**Inda ke da tsaga, sai a kara fadinta, sannan a karkare, a jika da ruwa, a dabe da kyau da jangargari**.

**b. Hutar itatuwa bisa dam**





**A hidda itatuwa, a tsabtace saman dam da gehenshi fadin metir 10.**

**Mayan itatuwa, wanda an kashe su sayunsu za su jayo matsala ga dam ana iya barinsu.**


.

c. **Kontawa ruwa bisa dam**





**Duk wurinda ya danfada a saman dam, sai a cike shi da jangargari, a jika da ruwa, kuma dabe shi da kyau.**

**d. Gina rijiya kalkashin waya na kawo faduwar dam**





- A kiyaye gina rijiya karkashin mabiyar ruwa. A cike tsohin riyoji
- Idan an gano zaizayar wuri a ketaran mabiyar ruwa, ana iya dabe wuraren kuma a cike su da mayan duwatsu..

**e). Hutar ruwakalkashin dam**





Idan an gano ruwa maras kyau na huta daga kalkashin dam a sannar da mahukunta ko kuma ma' aikata mai kula da ginegine.

**f). Hitar duwatsu**





Idan duwatsu na tsagar dam suka gushe, sai a karkare, a jika da ruwa, kuma a dabe da jangargari.




A kiyaye gina rijiya kalkashin dam.
A zan bunne tsohin rijiyoyin da ke karkashin dam da kusanshi.

**g). Zaizayewar dam**





A tsabtace, a jika da ruwa, kuma a dabe wurinda ya zaizaye da jangargari

A sake jera duwatsu.

**Hawan bisashe bisa dam**

A kiyaye biyar bisashe saman dam yau da kullum.



## VII. KAYAN AIKI DA KAYAN GUINI NA KULAWA DA DAM

### 1. Kayan aiki

Domin yin kananan ayoukan giara, komitin da ke koula da giare-giare ya kamata ya samu kayan aikin da ke biyowa :

- Hellu biyar (5) ;
- Diga uku (3) ;
- Kafin guina biyar (5) ;
- barro biyu(2) ;
- Bokiti biyu(2) ;
- Kangon tannao mai daukar lita 200 guda;
- Karamin hellu ta maguina biyu (2) ;
- Adda biyu (2) ;
- Rato biyu.

### 2. Kayan aikin guini

- Ruwa ;
- Kasa ;
- Tsakuwa ;
- Ciminti ;
- Jan gargari ;
- Duwatsuna ;
- Wayoyin keji